# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Yesu da Liyazarus



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**



**Wata rana,
Yesu ya wuce a cikin Yeriko. Wannan birnin ne Yoshuwa ya hallakar tun da. Yanzu mutanen da suke a wurin sun sake gina shi.  A cikinsu akwai wani mutum mai suna Zaka.**



**Watakila sauran mutanen da suke a Yeriko ba su so Zaka sosai ba saboda shi mai karbar kudin haraji ne daga garesu. Zaka ya aikar da wadansu kudaden ga gwamnati amma yakan ajiye sauran wa kansa.**

**Tun da shi mai karbar haraji ne, wannan ya sa yana da kudi sosai. Watakila gidansa ne ya BABBA kuma MAFI KYAU a wurin.**



**Amma shi gajere mutum ne sosai – amma ba gajere ne ga kudi ba, amma gajere ne a tsayi. Zaka bai yi girma kamar sauran mutane ba.**





**Sa’da da Zaka ya ji cewa Yesu yana a Yeriko, dan karbar harajin ya so ya ga Yesu Mutum daga Nazaret wanda ya ce Shi Dan Allah ne.  Amma taron jama’a sun yi yawa…mutanen kuma sun fi shi tsayi.**



**Zaka ya yi tunani!**
**Idan zan iya shan gaban**
**taron mutanen… in hau**
**kan itacen da yana**
**bakin hanya… zai**
**iya ganin Yesu.**



**Sai ya hau kan itacen Sikamo, Zaka ya sami wurin mai kyau tsakanin hannayen itacen sai ya zauna da kyau yana jiran Yesu. “Xan dube shhi da kyau,” watakila tunaninsa kenan. “Zan ga shi kuma babu wani wanda zai gan ni.”**

“Zaka, yi sauri ka sauka kasa.” Dan gajeren mai karbar haraji bai yarda da abin da kunnensa suka ji ba. Yesu ya tsaya a karkashin itacen. Yesu yan kallonsa. Yesu yana kiransa!





**Idan har Zaka ya yi mamaki da jin kiran Yesu, to babu shakka, ya fi jin mamaki sa'ad da ya ji Yesu ya ce, "Yau dole sai na zauna a gidanka." Zaka ya sauka daga itacen da sauri-sauri har ma ya kusa ya fadi.**

**Zaka ya ji dadi domin Yesu zai ziyarce shi a gidansa. Amma mutanen ba su ji dadi haka din ba. Suka yi gunaguni cewa Yesu zai ziyarce mai zunubi kamar Zaka.**





**Yesu ya kawo wani sabonrayuwa ga Zaka. Zaka ya ce, “Maigida, zan ba da rabi duka kayan da nake da shi ga talakawa. Kuma idan na cuce wani, zan mayar masa har sau hudu abin da na cuce su da shi.”**

**Yesu ya ji dadin sabon rayuwar Zaka. Yana so ya gan mutane suna tuba daga zunubansu su yi abin da ya dace. Yesu ya ce, "Dan Mutum ya zo ne don ya nemi ya kuma cece abin da ya bata." A ranar a Yeriko, Yesu ya sami Zaka.**



# Yesu da Liyazarus

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Luka 19**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

53

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**